


Karen Gidan Talaka

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:


Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.


Karen Gidan Talaka
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria


http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009







An yi wasu karnuka guda biyu.
Ɗaya na sama a gidan wani talakan manomi.
Ɗaya kuma na sama a fadar sarki.




Wata rana manomi da karensa sun je fada.
Manomi ya shiga gun sarki.
Ya bar karensa a waje




Karen fada ya zo gun karen manomi.
Karen fada yana taƙama da samansa a fada.
Yana cin daɗi yana kuma kwanciyar daɗi.
Karen manomi ya ce ya gode Allah.
Yana cin abin da Allah ya ba manomi.



Suna cikin hira sai ɗan sarki ya fito.
Ya wurga sanda da nisa.
Karen fada ya tashi da gudu.
Ya je ya dawo da sanda.
Ɗan sarki ya sake wurga sanda da nisa.
Karen fada ya gaji tiliz.



Manomi ya fito daga wurin sarki.
Ya shafe kan karensa.
Ya kuma ba karensa ragowar nama.



Karen manomi ya juya ya dube karen fada.
Yana kan gudu ya kawo sanda.
Karen manomi ya ce wanan wahala ne.
Ya gode Allah shi ba karen fada ba.



Karen manomi ya lashi ƙafar manomi.
Manomi ya shafa kan karensa.
Suka koma gida tare suna hira.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK